BA A MAGANCE BARNA DA BARNA: NAZARIN MATSALOLIN ZANGA-ZANGA A CIKIN WASU RUBUTATTUN WAQOQI NA HAUSA

Daga

1. Ibrahim Baba (Nayaya)[1] PhD in view
National Teachers Institute, Kaduna.
+2347066366586/ +2348125351694
ibrahimba182@gmail.com

Da

Danlami Bala Gwammaja, PhD
Aminu Kano College of Islamic and Legal Studies, Kano
08020605148 danlamigwammaja@gmail.com

Da

Binta Bala Kwaru
Department of Hausa, Aminu Kano College of Islamic and Legal Studies, Kano 08069612984 bintabalakwaru@gmail.com

Tsakure
Duk wani abu da ya faru, mai kyau ne ko akasin sa, to akwai dalili! Tabbas haka abin yake a zamantakewar rayuwar al'umma. Wata rana, rayuwa ta yi fari, wata rana kuma ta yi baqi. A wannan takarda, ta yi qoqarin fito da bayanai a kan zanga-zanga daga cikin wasu waqoqin Hausa rubutattu. A binciken, an yi qoqarin nazartar waqoqi guda biyu, inda a cikinsu aka zaqulo wasu baitukan da suka yi Magana a kan sabuban zanga-zanga, da hasashen yadda ake gudanar da zanga-zanga, sannan da matsalolin da zanga-zanga kan iya haifarwa. A takardar, an fara bijiro da ma'anar waqa da taqaitaccen tarihinta, sannan aka biyo baya da tarihin samuwarta. Har wa yau dai, binciken ya zo da bayani a kan ma'anar zanga-zanga, raberabenta da kuma illolinta, inda takardar ta fi mayar da hankali a kan zanga-zangar da ba ta lumana ba. A yayin gudanar da binciken, za yi qoqarin bin ayyukan masana waxanda suka jivinci wannan aiki, da kuma kallon yanayin da ake ciki, tare da bibiyar al'amuran tsaro da tsadar rayuwa. Babbar manufar takardar dai, fito da zahirin rayuwar al'umma daga cikin ayyukan adabi, da kuma nuna yadda adabi ya zama haske ga rayuwar al'umma kai tsaye. A qarshen takardar, an bayyana sakamakon da binciken ya gano, sannan aka zo da kammalawa. An xora wannan aiki a kan ra'in Mazahabar Nason Adabi a Aladu (Folk-Cultural Theory) wadda William Bascom (1912 – 1981) ya qirqira.
Kevavvun Kalmomi: Magance, Varna, Matsaloli, Zanga-Zanga, Sababi, Rubutattun Waqoqi

1.0 Gabatarwa

Waqoqi a wurin kowace aba ce mai muhimmanci, sannan wata kafa ce ta isar da saqon da ake son jama‘a su sani. A cikin waqa, akan nusar da al‘umma ire-iren matsalolin da suka addabe ta; da kuma zayyano hanyoyin mazaye waxannan matsaloli, kamar yadda kuma a cikin waqar akan bayyana wata nasara da al‘umma ta samu. Al‘ummar Hausawa suna daga cikin waxanda suka xauki waqa da muhimmanci, da ita suna isar da saqonninsu tun a jiya, har yau da aka samu sabon zubi a tsarin waqoqin, imam dai
rubutattu ne da kuma na baka.

A wannan takarda, an yi qoqarin zaqulo wasu waqoqiguda biyu waxanda dukkaninsu rubutattu ne waxanda suka bayyana matsalolin da zanga-zanga takan iya haifarwa, inda marubutan suka buga misalai daga irin abubuwan da zanga-zangar ta haifar a wannan Qasa ta Nijeriya.

1.1 Rubutacciyar Waqa

Masana sun yi qoqarin bayyana ma‘anar waqa; imma dai ta baka ce ko kuma rubutacciya. Amma a nan, za mu taqaita wajen kawo ma‘anar rubutacciyar waqa kawai. Yahaya (1976:1) ya ce:

> ―Waqa magana ce ta fasaha a cure wuri xaya a cikin tsari na musamman‖.

Shi kuwa Umar (1980:3) cewa ya yi:

> ―Waqa tana zuwa ne a sigar gunduwoyin zantuka waxanda ake kira baitoci ko xiyoyi kuma ake rerawa da wani irin sautin murya na musamman‖.

Xangambo (2007:6) kuma ya ce:

> ―Waqa wani saqo ne da aka gina shi kan tsararriyar qa‘ida ta baiti, xango, rerawa, kari (bahari), amsa-amo (qafiya), da sauran qa‘idojin da suka shafi daidaita kalmomi, zavensu da amfani da su cikin sigogin da ba lalle ne haka suke a maganar baka ba‖.

Shi kuma Yahya (1997:2-3) cewa ya yi:

> ―Waqa maganar hikima ce da ake rerawa ba faxa kurum ba wadda ke da wani saqo da ke qunshe cikin wasu kalmomi zavavvu, tsararru, kuma zaunannu‖.

A dunqule, ta la‘akari da yadda masana suka kalli ma‘anar waqa, za mu iya cewa, waqa tsararriyar magana ce da ake yin ta cikin hikima da zavin kalmomi, ba kara zube ba, domin isar da saqo ko wata manufa ga al‘umma.

1.2 Tarihin Samuwar Rubutacciyar Waqa

Rubutattun waqoqi sun samo asali ne daga waqoqin Larabawa (Yahaya da Dangambo, 1986). Waqoqin Hausa na farko an rubuta su ne a cikin Hausa ajami. Haka kuma, su waxannan waqoqi duk sun wanzu ne sakamakon addini. Wato, abin nufi a nan shi ne, qoqarin yaxa addinin Musulunci shi ne ya haddasa kuma ya havaka rubutattun waqoqi na Hausa. Ana zaton cewa, waqoqin sun faro daga lokaci mai tsawo da ya wuce, wato tun lokacin da Musulunci ya yi qarfi. Akwai zancen cewa, rubutattun waqoqi sun faru tun qarni na 17 da na 18[1], kamar yadda tarihi ya nuna[2]. Abin da yake tabbas shi ne cewa, rubutacciyar waqa ta havaka ne a qarni na 19, wato zamanin jihadin Shehu Usmanu Xan Fodiyo.

Waqoqin Qarni Na Sha Tara

A wannan qarni na sha tara, an sami wani yunquri na bunqasa ilimi, da yaxa addinin Musulunci, da kau da jahilci da al‘adu, da camfe-camfe a qasar Hausa. Shugabannin jihadi sun yi wallafe-wallafe masu ximbin yawa na fannonin ilimi daban-daban da Larabci, kamar su Tauhidi da Fiqihu da Hukunce-Hukuncen Shari‘a da tsarin mulki da dai sauransu. Daga nan suka ga cewa, hanyar da ta fi sauqi ga isar da saqonsu ga jama‘a, ita ce ta hanyar harshensu. Suka ga kuma cewa, waqa ce ta fi sauqin shiga kai, sai suka shiga bayyana musu manufofinsu a waqe da Fillanci da kuma Hausa, suna tsamo waxannan manufofi nasu daga cikin talifan da suka yi da Larabci (Abdulqadir, 1979).

Shehu Usmanu da Abdullahi qanensa da Nana Asma‘u da Isan Kware _ya‘yansa da wasu daga cikin almajiransa irin su Mamman Tukur da Dikko Xanbagine da Gixaxo xan Lema, duka sun rubuta waqoqi masu yawa da Hausa. Daga cikin waqoqin da suka rubuta akwai _Waqar Tabban Haqiqa‘ da _Waqar Lalura‘ da Waqar na Shehu Usmanu Xan Fodiyo. Sannan kuma, akwai _Waqar Tsarin Mulki na Musulunci‘ da _Waqar Murnar Cin Birnin Alqalawa‘ na Abdullahi Xan Fodiyo. Haka kuma, Nana Asma‘u ta rubuta waqoqi irin su _Godaben Gaskiya‘ da _Tawassuli‘ da _Kirarin Amada‘ da _Roqon Ruwa‘ da _Sharuxxan Qiyama‘. Shi kuwa Isan

[1] Wato kamar waqoqin su Muhammadu Alkatsinawi da Muhammadu Na Birnin Gwari da Malam Shi’itu Xan Abdurra’ufu, irin su Gangar Wa’azu/Bakandamiya, da Waqar Wawiya, da Waqar Jiddul Ajizi Ba’ajamiya, da sauransu.

[2] Kamar a cikin littafin Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa na Ibrahim Yaro Yahaya (1988).

Kware ya rubuta _Waqar Haqqin Mumini Bisa Mumini‘ da _Waqar Tarbiyyar Yara‘. Haka Mamman Tukur ya rubuta _Waqar Baqin Mari‘. A taqaice dai, Shehu Usmanu Xan Fodiyo da mutanensa sun rubuta waqoqi masu a wannan qarni na 19[3].

Yawancin waqoqin qarni na 19, an rubuta su ne kan yabon Ubangiji da yabon Annabi da wa‘azi da fiqihu da shari‘a da sha‘anin mulki. Wato dai jigonsu ya fi ba da qarfi ga addini. Wannan bai canja ba har zuwa qarshen wannan qarnin, da ma farkon qarni na ashirin.

Waqoqin Qarni Na Ashirin

A cikin qarni na ashirin an samu wani sabon salo na rubuta waqa a qasar Hausa. Sarkin Zazzau Aliyu Xansidi shi ya fara buxe qofar wannan qarni da waqarsa ta habaici mai suna _Tabarqoqo‘ (Abdulqadir, 1979). Mun ce waqoqin qarni na sha tara kusan sun qunshi addini ne kawai, to amma a qarni na ashirin sai aka sami wasu waqoqin da suka shafi rayuwar xan‘adam ta yau da kullum, bayan na addini. Da farko dai, a wannan qarni jigon addini ya ci gaba. Sannan kuma, an sami waxansu jigogi daban-daban da ba na addini ba. Waxannan jigogin sun haxa da siyasar jam‘iyya da soyayya da al‘adu da wayar da kai da kishin qasa da kishin harshe da gargaxi da faxakarwa da nasiha da ta‘aziyya da nuna hikima da dai sauransu da yawa.

1.3 Dabaru da Hanyoyin Bincike

Duk wani bincike da za a aiwatar ko aka aiwatar, dole ne a samu cewa an yi amfani da wasu dabaru da kuma bin wasu ayyanannun hanyoyi domin aiwatar da shi. Yayin gudanar da wannan bincike, an yi qoqarin amfani da sauraron bibiyar lamarin zanga-zanga da ta afku a wasu sassa na wannan qasa, sannan aka karanta tare da sauraron rerarrun waqoqin baka da suka shafi zaman lafiya, sannan aka bibiyi wasu rubutattun ayyukan adabi.

1.4 Ra’in Bincike

A dukkanin binciken da ake yi na ilimi to dole ne a samar masa da maxosa, wato ra‘in da wannan binkice zai jinginu zuwa gare shi. Wannan nazari ya sami tagomashin xoruwa a kan ra‘in Mazahabar Nason Adabi a Aladu[4] wadda cikin mabiyanta akwai William Bascom (1912 – 1981). Wannan Mazhaba tana kallon yadda hikima da sauran dabarun fasahar baka suka danganci abubuwan da al‘umma suke gudanarwa. Har wa yau, Mazahabar ta faxaxa zuwa ga

[3] Don qarin bayani duba Gudummawar Masu Jihadi Kan Adabin Hausa (Juzu’i Biyu), Kundin Digiri na Biyu na Bello Sa’id, 1978. Ko Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa na Ibrahim Yaro Yahaya, 1988.

[4] Folk-Cultural Theory

abubuwan da suka danganci fasahar zamani ta amfani da na‘urorin kwamfuyuta wajen alaqanta maganganun adabi da al‘adu. Ana amfani da wannan ra‘i wajen nazarin al‘adu na Hip-Hop da rawar disco da rawa ta masu nuna

tsiraici da al‘adun da ake amfani da su wajen shirya finafinai a Amurka (Gusau, 2015).

2.0 Ma’anar Zanga-zanga

A xaya-xayar ma‘ana ta zanga-zanga, za a iya cewa, fitowar al‘umma qwansu da qwarqwatarsu domin nuna damuwa kan wani abu da ba su yarda da shi ba wanda masu mulki ko wasu ayarin jama‘a ke gudanarwa, amma mahukunta sun kasa tsawatar musu. Irin wannan yanayi, kan sa a fito domin yin koke ga shugabanni domin su gyara, ko kuma su sauqa a kan mulki, idan su aka yi wa. Sai dai a yau, zanga-zanga na bayuwa zuwa ga ta‘addanci, da sacesace, da qone-qone har ma da asarar rayuwa tsakanin masu yi da jami‘an tsaro.

2.1 Ire-iren Zanga-zanga

Idan aka kalli tsarin gudanar da zanga-zanga tsakanin al‘umma, za a iya kasafta ta zuwa gida biyu manya, wato zanga-zangar lumana, da kuma zanga-zangar ta‘addanci wadda galibi ita ce abar tsoro, kuma it ace wadda a yau ta fi shuhura a yankunanmu.

2.2 Illoli da Amfanin Zanga-zanga

Iri zanga-zangar da ake yi a yau, tana da illoli da haxura da dama, musamman la‘akarida yanayin al‘umma da kuma yadda aka fahimce ta ba bisa yadda take ba. Wasu

daga cikin illolin sun haxa da:

- Asarar rayuwa, ta hanyar fito-na-fito da jami‘an tsaro, ko kuma ta kaure ta koma faxa tsakanin masu gudanarwa.
- Asarar dukiya, ta yadda ake qone-qone da sace-sacen dukiyoyin al‘umma da na gwamnati. Sannan a wannan gavar, akwai lalata kayan gwamnati ta hanyar ruguzawa da qonewa.

3.0 Sabuba da Matsalolin Zanga-zanga a Wasu Rubutattun Waqoqin Hausa

Kamar yadda aka gani a taken wannan maqala, takardar tana magana a kan sabuban da suke sanya a yi zanga-zanga, da kuma bayyana yadda a yanzu zanga-zangar ka iya kasancewa, sannan da kuma matsalolin da zanga-zangar takan iya haifarwa, musamman wadda take ba ta lumana ba.

3.1 Sabuban Zanga-zanga a Wasu Rubutattun Waqoqin Hausa

A wannan gava, an yi qoqarin kawo wasu baituka daga waqar _Zanga-zanga‘ ta Bunza, waxanda baitukan ke xauke da sabuban da suke sanyawa a yi zanga-zanga. Ga abin da ya ce:

Manufar zanga-zanga taho kusa in faxa ma,
Al‘umma su taru gu xaya don nuna qyama,
Tun daga shugaban qasa, gwamna zuwa ciyama,
Da talakkan qasa da sarki, dagaci, ciroma, Duk
su fito su nuna haushi na rashin kulawa. A fito
zanga bur babu tsoro ga ni ga ka,
A karanto dalilan da munka ga ba mu son ka,
Da sharuxxan da in an amince ba mu qin ka,
In ta buwaya tilas burabus ko a sauqa, Ai
taron qasa don a gayyato mai iyawa. In fa
talakka ya gane gwamnati ba ta son sa,
Ba ta kula da shi duk abin da ya zo a kansa,
Yai fatara da ragga a bar shi cikin fasonsa,
Yai kuka ya quwata ko kuwa ba su jin sa, Gwamnati na
gani talakkawa na macewa.
Mai noma ana gani yunwa na kashe shi,
Ya cinye iri da wainar ya bai wa mai shi,
Yau naira dubu da qari aka sai da kyan shi,
An manta da magganar gyara wa ga qyashi,
Mun ji musabbabin zanga-zanga ba musawa.
Malamman firamare an gaza agazar su,
Su na sakandare tuntuni an bar kula su,
Manyan jami‘o‘inmu an yi kusan rufe su
In ko sun yi yaji a ce ba a biyan su, Matsalolin
ga zanga-zanga suka haddasawa.
_Yansandan qasa ta‘addanci na kashe su,
Sojojin tsaronmu _yan bindiga na tsare su,
SSS su kai rahoto ba a kula su,
EFCC na cikin aikin a hana su, To ga
zatonku me rage in bayan varewa.
Babu ma‘aikacin da bashi bai qwazzaba ba,
Babu garin da _yan gudun hijira ba su dire ba,
Babu jihar da _yan samame ba su kai hari ba,
Maganar gaskiya kan tsaro ba a san ta yi ba,
Kurar kardi ce da kowa ciki ba rabewa.
Mummunan talauci haqiqan ya riqe ku,
Gwamnati ta yi tallafi bai kai wa a gunmu,

Cin hanci da maguxi sun jujuta kanmu, In fa
talakka ya ga ba makawa za shi ji mu, Bore
za shi yi walau nasara ko macewa.
Albashin ma‘aikata ba sai na faxi ba,
Ya zama xan tukuici kamar dai ba biya ba,
An yi zaman a gyara shi gwamnati ba ta kula ba,
Dole su garzayo shiga bore ba da so ba, Wa
zai haquri da cuta ta daxin-daxawa.
In ka je a kasuwa ga tsada da cuta,
Ga algushu tauye ma‘auni ga matsata,
Mabarata da _yan ba mu maula ba misalta,
Marasa sun tuqe qasa ba mu da
In aka ta da zanga-zanga wa zai hanawa.

(Bunza, baiti 3 – 12). A waxannan baituka, an ga yadda Mawaqin ya yi qoqarin sarrafa fasaharsa wajen fito da sabuban zanga-zanga, inda ya yi qoqarin bayyanawa cikin baituka goma. A ciki, ya bayyana munanan halin da al‘umma ta samu kanta, wanda duk inda aka samu haka a tsakanin al‘umma, to tunaninta shi ne a fito a yi zanga-zanga domin samun mafita.

3.2 Hasashe da Yadda Ake Gudanar da Zanga-zanga a Wasu Rubutattun Waqoqin Hausa

Kamar yadda aka sani, irin wannan zanga-zangar ta ta‘addanci, takan haifar da wasu matsaloli waxanda kan sanya jama‘a zaman zullumi da firgici da asarar dukiya da asarar rayuka, har ma da sama da waxannan. Marubuta waqoqin Hausa ba su bar fagen haka ba, domin sun yi tsinkaye kan faruwar hakan, wannan ya sanya suka bayyana yadda ya kamata zanga-zangar ta kasance gudun kada a samu ta juyo ta koma ta‘addanci. A waqar Bunza (2024) ya yi qoqarin bayyana hakan. Ga abin da ya ce:

In tura ta kai ga bango ai anniyarta,
Ba a barazana da tsauri don shawo kanta,
Matsala ta game qasa kowa na tsakanta,
Ba makawar faxinta kowa ya ji sassalarta
Yin haka bai zamo haramun ba ga tsawatawa.
Ga wani hanzari _yan‘uwana ba gudu ba,
Sai a yi hattara zanga-zanga ba faxa ba, Ba
a zage-zage ba a tsine wa babba, Ba a
cin ido da cin fuska ba a gaba,
Sai a kula da _yan zuga masu bixar zaqewa.
A faxi gaskiya free parlor babu tsoro,
Don manya su ji wa kunnensu su xauki horo,
A ji muryar talaka shi ne manufa ga taro,

Ai a cikin yabanya ana iya gane gyauro, Sai
a cire a qwalqwale tausa bai tsiro ba.
Ba a ihe-ihe ba fitina babu darga,
Ba a kixa bare rawa wane yaga riga,
Hana jama‘a fita larura wacce hakan ga, Manufar
zanga-zangar lumana gyara jinga, Ba da riqon
qasa ga masu kwatanci iyawa. To hayyar ku
ga vata gurbi a zan ka lura,
Muggan _yan siyasar da anka kasa ga tsira,
Za su gudunmawar tallafi don ta da qura,
Tare da su qasar nan ta durqusa tun a bara,
Matsalolinmu gadonsu anka yi tun daxewa.
Bambanci na masu addinan salsala ce,
Sa shi cikin batun zanga-zanga yaudara ce, In
matsala ta shafi addini guguwa ce, Kan a kashe
ta hankalin kowa zai ximauce, Ai
ta kisan talakka to kun ji daxin daxawa. Kada
ku aminta vangaranci ya shigo cikin nan,
Ba wani vangaren da babu macuta wurin nan,
Matsalar rayuwa ta game kowa qasar nan, Don
haka babu vangaranci bisa yunqurin nan,
_Yan kicihen rabon qasa nan suka lallavowa.
Duk tsarin da _yan qabilanci sun ka shirya,
Sai sun sakaxo munafuccin ta da ya ya,
Kar ku aminta ko sun fito gayya da gayya,
Masu jira qasa ta koma wasat tawayya,
In suka kutsa kai qasa suka so wargajewa.
Ya ya za a zanga-zanga a ga fa‘idarta,
Tun farko a xauko doka a yi fassarar ta,
Wac cancanci shugabanci bisa qa‘idar ta,
Wa ya kamata ai zanga-zangar bai riqonta,
Mun yi hawan zanga-zanga bai fitowa.
Tilas ne mu nuna qyamar mu ga masu
zamba,
Mu quri‘ar a sake shiri tun ba su gama ba,
Se a mayar da su gida tun ba su kai garas ba,
Babu taqaddama jinin kowa bai zube ba,
Ba sai soja ya yi kutsa ba muna
iyawa.
Wani kwamitin riqon amana duk ba mu son sa,
Party ko wane iri mun kafirce yin sa,

Duk tsohon maci amana ya bi aniyarsa, Yara, maza da mata da
tsofaffi matasa,
A yi _yartinqe mai yi free ba mai rabawa.
Sai a yi gwari-gwari ba harsashen da sanxa,
Masu riqon qasarmu sun kasa dole yarda,
Ga yunwa rashin tsaro komai ya yi tsada,
Matsanancin talauci qishirwa babu randa,
Ba mafita ga wanga tsari face macewa.
Bishiyar dikku _yan siyasa a ganin mutane,
Se ku yi hanzarin murabus ku fice birane,
Hanya babu kyau dole za a varin tukwane,
An kai intaha yanzu sai dai nunenune, An
gama sa zare me rage illa karawa.
Se ku yi hattara qasashenmu na qetarenmu,
Su ke ture _yan ta‘addar da suke kasha mu,
Duk wani gangamin wakilansu suna ishe mu,
Su yi ka‘in da na‘in cikinmu suna zuga mu,
Tarzomar rashin hankali suka assasawa. Mun
sa an kasha qasa an ka ruhe lagonta, An wa
arzikin qasa wasoson mugunta,
_Yan hana _yan qasa haxin kai aikin nagarta,
An shiri yau biri gas hi cikin asunta, Se _yan
soshe-soshe fuska na tamurewa.
Burin _yan qasa abinci ya wadata sosai,
Albashi ya ci da mai shi daidai cikin shi,
In haka ta kasance tsaro zai samu sosai,
Aikin yi a hankali kowa na riqo nai, Yin haka
xai ka sa zanga-
zanga wargajewa.
Na dai yadda tabbas siyasa qaddara ce,
Ta ci talakka ta sa sarakai sun yi kwance,
Ta ma malamai bugun shar sun ka sa zance,
Tajirai da filin Ta‘ala sun tsiyace,
_Yan boko da manyan takardu bai musawa.
Kan mu yi zanga-zangar akwai darasin kulawa, Tare da
wa muke yi ga wa kuma za mu yo wa,
Su dai _yan siyasa bazarmu suke rayawa,
_Yan boko cikinsu duk mu ne ba rabawa, Kar fa
mu kai talakka kurmindi mai nutsewa.
In abu ya vace hankali ai bai vata ba,

Rago in ya ja baya ba tsoro ya sa ba,
Sake shirin karafkiya ne a fage na gaba,
In aka bar ma‘aikata ai ciki bai yi kyau ba,
In aka bar wa _yan siyasa ba sa iyawa.
Ga alama fa zanga-zanga dai za a yin ta,
Matsalolin qasa ya sa dole ake gwada ta,
Matuqar an gwata an kai nasara a kanta,
An gama karya _yan siyasa da mazan jiranta,
Kowa hau kujera kamar ta ake riqewa.

(Bunza, bt: 16 – 35).

A waxannan baitoci, Mawaqin ya yi qoqarin fayyace yadda ake gudanar da zanga-zanga, da kuma yin hannunka mai sanda ga jama‘a a kan kada su yarda a yi amfani da sunan zangazanga a tayar da hankalin al‘umma. A ciki dai, ya bayyana yadda muggan _yan siyasar da su aka lalata qasar, amma yanzu tunda ba da su ake damawa ba, to a yi hankali da su, gudun kada su fake da zanga-zanga su zuga talakawa domin su yi qone-qone da sauran ayyukan ta‘addanci.

3.3 Matsalolin Gudanar da Zanga-zanga a Wasu Rubutattun Waqoqin Hausa

Bayan bayyana sababin aiwatar da wani abu, yana da kyau a kawo yadda ake yinsa, yayin da aka kauce wa tsarin gudnarwa kuwa, babu shakka za a gamu da matsaloli, to idan kuwa na gamu da su, to fa fito da su sarari domin a gansu abu ne mai kyau. Kamar yadda aka sani, marubuta da mawaqan Hausa ba a bar su a baya wajen yin hakan ba, don a nan, za a koma ga wata rubutacciyar waqa domin zaqulo wasu baituka da aka bayyana haxarin zanga-zanga; musamman irin wadda ake aiwatarwa a yau. Marubuci Nayaya (2024), ya kawo ire-iren waxannan matsaloli a cikin waqarsa mai suna _Haxarin Zangazanga‘. Ga baitukan da ya ambaci illolin:

Zanga-zanga 'yan'uwana,
Ce masifa ce ga juna,
Ta kashe mai rai da rana.
In ko kun ce maffita ce,
Har nufatar za ku qwace, Zo na shaida ma zance.
Lura yau rikicinta qaru, An kashe rai an fa qwaru,
Dukiyar wasu sun asaru.
An yi sata an yi qone,

An saka mu gida mu zaune, In da mai
qi za a zane.
Kasuwanni an rufewa,
Bankuna duk babu kowa, Har ibada ba
fitowa.
Ga school an garqamewa,
Ba travel ko matsawa,
Jami‘ai ke zane kowa.
Duk dalilin zanga-zanga,
Wanda kunka fito da burga, Mun faxa kun
kasa hanga.
Yau ina sauran aminci, Ko
sukunin yin zumunci, Babu
damar cin abinci.
Babu barci don sukuni,
Tunda an kauce tunani,
Kun zata kwa fid da
raini. Ga jidali an saka mu,
Mun shige wahala da kanmu,
Babu mai jin qorafinmu.
Ya matashi ba ni kanka,
Ba a zafin kai a harka,
Za a kai qarshen batunka.

A waxannan baituka kuwa, an yi qoqarin bayyana yadda zanga-zanga ta mayar da al‘umma bayan aiwatar da ita, inda a ciki aka nuna cewa zanga-zanga a sanadinta an yi kasha-kashe, an yi qone-qone, an yi sace-sace, an yi rushe-rushe da sauran muggan ayyukan da suka zamto lalata dukiyar al‘umma da kuma varnatar da kayan gwamnati ne.

4.0 Sakamakon Bincike

Duk wani abu da za a gabatar, to fa la-shakka za a samu sakamako, walau mai kyau ne ko kuma akasin haka. Wannan maqala, ta yi qoqarin gano sakamako kamar haka: Fito da hangen nesa na Bahaushe, musamman marubuta waqoqin Hausa.

- Alaqar adabi da rayuwar al‘umma, ta yadda akan yi hasashe da kuma bayyana yadda za su gudanar da rayuwarsu a tsarin adabi.
- Kaifin hikimar marubuta, ta yadda suke fayyace duk wata matsala a cikin tsarin waqa.

4.1 Kammalawa

Qarshen tika-tika-tik, wannan maqala an qwalqwale ta bayan zubo bayanai da ma‘anonin waqa da zanga-zanga da kumaillolinta. A maqalar, an ga yadda marubutan suka bace basirarsu wajen qulla zaren tunaninsu yayin rubuta waqa. An fito da sakamako, sannan aka rufe da taqaitaccen bayanin kammalawa.

Manazarta

C.N.H.N. (2006) Qamusun Hausa Na Jami'ar Bayero. Zari a: ABU Press.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero Kano (1979) Waqa A Bakin Mai Ita. Littafi Na Biyu. Zaria: Northern Nigerian Publishing Company.

Cibiyar Nazarin Hausa, Jami'ar Usmanu Danfodiyo Sakkwato (2006) Bargon Hikima: Diwanin Waqoqin Xangaladiman Wazirin Sakkwato Alqali (Dr.) Muhammadu Bello Gixaxawa. UDU Press.

Cibiyar Nazarin Hausa, Jami'ar Usmanu Danfodiyo Sakkwato (2006) Gizama Gogan Waqa: Diwanin Waqoqin Alhaji (Dr.) Umaru Nassarawa Wazirin Gwandu (1916 – 2000). UDU Press.

Xangambo, A. (2007) Xaurayar Gadon Fexe Waqa: Sabon Tsari. Kano: KDG Publishers.

Umar, M.B. (1980) Nazarin Waqoqin Hausa. Zariya: Hausa Publications Centre.

Yahaya, I. Y. (1988) Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa. Zaria: Kamfanin Buga Littattafai Na Nigeria Ta Arewa.

Yahaya, I. Y. da Dangambo, A. (1986) Jagoran Nazarin Hausa. Zaria: Northern Nigerian Publishing Company.

Yahya, A. B. (1997) Jigon Nazarin Waqar Baka. Kaduna: Fisbas Media Services.